## SŪRATUL FĪL سُورَةُ الفِيلِ

Tana nūna darajar Hurumin Makkah, yadda Allah Yake halakar da mai nufinta da yāƙi ko wani sharri.

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

*Da sūnan Allah, Mai rahama, Mai jin ƙai.*

1. Ashe, ba ka ga yadda Ubangijinka Ya aikata ga mutanen giwa[1] ba?

أَلَمْ تَرَ كَيْفَ فَعَلَ رَبُّكَ بِأَصْحَٰبِ ٱلْفِيلِ ﴿١﴾

2. Ashe, bai sanya kaidinsu a cikin ɓata ba?

أَلَمْ يَجْعَلْ كَيْدَهُمْ فِى تَضْلِيلٍ ﴿٢﴾

3. Kuma Ya sako, a kansu, wasu tsuntsāye, jama'a-jama'a.

وَأَرْسَلَ عَلَيْهِمْ طَيْرًا أَبَابِيلَ ﴿٣﴾

4. Suna jifar su da wasu duwatsu na yumɓun wuta,

تَرْمِيهِم بِحِجَارَةٍ مِّن سِجِّيلٍ ﴿٤﴾

5. Sa'an nan Ya sanya su kamar karmāmi wanda aka cinye?

فَجَعَلَهُمْ كَعَصْفٍ مَّأْكُولٍۭ ﴿٥﴾

---

(1) An yi Yāƙin Gīwa shēkarar haifuwar Annabi, tsakānin halaka su da haifuwarsa kwāna hamsin. Bayan shekara arba'in Annabi ya fara karantar da mutane. Ya karantar da su cikin shekara ashirin da uku, sa'an nan ya ƙaura. Bayansa da shekara hamsin waɗanda suka bi shi suka cinye duniya. Wannan yana nuna cewa mutane ba su samun daraja sai da riƙon addini da ilimi.